# YIN TAFIYA CIKIN JIRGIN KASA NA MUTUWA

## (Sako Mai Kawo Bege)

Moses C. Onwubiko

Ne ya rubuta

"Ba Kaunar da ta fi haka Ga Mutane, wato mutun ya
Ba da ransa saboda aminansa"
(Yahaya 15:13)

Yi tunani kamar haka, cewa kana cikin wanda ya kama hanya zuwa wurin da ake kashe mutane. Duka wadanda suke cikin jirgin harda kai ma, dukan ku, an yanke maku hukuncin kisa, za' a kai ku wurin da za' a kashe ku kenan.

Lokacin da jirgin ya kusa da wurin kisa sai aka hangi wani saurayi a tsaye, a tsakiyar hanyar jirgin yaya daga Jar – tuta, yana so jirgin nan ta tsaya, da kyar mai tukin jirgin ya yi kokari ya sa jirgin ta tsaya. Masu lura da jirgin kuwa suka yi sauri suka je wurin saurayin nan don su tanbaye shi dalilin da ya sa, ya tsayar da jirgin, suka kuwa ji dalili, cewa domin shi saurayin yana so ya mutu a madadin wayenda su ke cikin Jirgin. "Inna nan domin in hana kisan da za a yi" Saurayin ya fadi haka ne ba tare da tsoro ba. Masu lura da Jirgin, kowa cike da mamaki, nan da nan suka sanar wa alkalin da ya yanke hukuncin, abinda ya faru.

Bayan alkalin ya dauki lokaci mai tsawo yana masa tambayoyi, sai alkalin ya barshi ya dauki hukuncin wadancan mutanen, domin bai taba yin laifi ba bisa ga rahotani da aka bayas akansa, ba shi da laifi ko daya; amma kuma ya ba da kansa don ya dauki hukuncinsu.

## Ya Nuna Kaunar da Yake Da Ita Domin Masu Laifi

Yayin da kai da duk sauran jamma'a suke kallo, aka tafi da shi don a Kashe-shiru. Aka ba shi wahala aka wulakanta shi a madadin duk wadanda suka yi kusa da mutuwa. Ina so ka dauki lokaci ka yi tunani game da wannan abu da ya faru. Abin ya fi karfi genewar mutum cewa wani zai mika kansa duka domin ya dauki horon laifin wadansu.

Yayin da saurayin nan mara laifi yake rataye a inda ake kashe masu laifi, ya tada murya da karfi ya yi kira domin taimako, amma ba wanda zai taimake shi. Daga karshe kuwa ya ja numfashinsa na karshe. Don me haka ya faru? Domin mutanen da suke cikin Jirgin mutuwa su tsira. Alkalin ya ba da sharadi guda daya game da abinda mutenen cikin Jirgin zasu yi kafin su samu tsira da mutumin nan ya kawo masu ta wurin ba da ransa domin su.

## Gaskiyar Ita Ce

Wannan ba labara ba ne kawai, an kamanta ne. Littafi mai tsarki ta bayana a fili Cewa:

> Gama yan adam duka sun yi zunubi, sun kasa kuma ga daukakar Allah (Romawa 3:23).
>
> Gama sakamakon zunubi mutuwa ne (Romawa 6:23a)

Wannan hukuncin da aka yanke daga babbar kotun sama, ya nuna cewa kowa mai zunubi ne kuma dole kowa a jefa shi cikin gidan wuta a rabe da Allah har abada kowa da kowa yana karkashin hukuncin Allah – a cikin Jirgin kasa na mutuwa ta har abada.

## Kokarin Dan Adam

Littafi mai tsarki ta karyata duk kokarin da mutum keyi don ya wanke kansa gaban Allah. Wani zai iya cewa, "To,ina Kokari yin abubuwa nagari" littafi mai tsarki ta na cewa:

> Babu wani mai aiki nagari, babu ko da guda daya (Romawa 3:12b)

Missing Sentence?? Duk da haka wani zai nace cewa “Ina ta kokarin kiyaye dokokin Allah. Har yanzu dai Littafi mai Tsarki tana da amsa domin:

> Duk wanda ke kiyaye dukkan shari’a amma a saba kan abu guda ya saba shari’a gaba daya kenan (Yakub 2:10).

Tambaya ita ce : Dokokin Allah guda nawa ne dole mutum ya kiyaye su kafin ya samu karba a wurin Allah har ya shiga sama? Dukan su! Karya doka daya,ya nuna ka karya dukan sauran dokokin kenan (Yakub 2:10). Wanene zai iya kiyaye su duka” wanene zai iya gama yini guda, ko sati, ko kuma shekara ba tare day rashin biyayya da dokokin Allah ba? Gaskiyar ita ce:

> Babu wani mai adalci, babu ko daya (Romawa 3:10b).

Kila wani zai nace cewa yana ko kuma tana kokari, amma Littafi, Mai tsarki na cewa

> Dukanmu muka cika da zunubi har ayyukanmu mafi kyau kazamai ne duka (Ishaya 65:6a)

Ba shaka wannan ba labara mai dadi ba ne ga kowa duk kokarin dan adam yake yi don ya samu shiga wurin Allah an ce ba wanda ya isa. Me muke da shi kuma?

**Babu Kome!**

Ko Yadda Allah ya karyata duk kokarin dan adam ya sa ke nan ba dan adam da zai iya shiga sama? Babu. Abin nufi shi ne duk kokarin mutum banza ne. Begen da muke da shi: maganin wahalarmu shi ne Alherin Allah.

## Dan Adam Cikin Mawuyacin Hali

Ubangiji Allah mahallici shi mai tsarki ne, shi cikakken mai adalci kuma mai shari'a gaskiya. Cikin tsarkinsa ba zai iya wata dangantaka da zunubi ba (1 yahaya 1:5). A matsayinsa na Allah mai gaskiya, ba zai ya ki bada horo domin zunubi ba. Babu yadda mutum mai kasawa zai yi dangantaka da Allah cikakke marar zunubi. Ba Zai taba yiwuwa wurin kokarin Mutum ba.

> Ga mutane, ba mai yiwuwa ba ne, amma gun Allah kowane abu mai yiwuwa ne (Matiyu 19:26b)

Saboda haka mutum ba zai taba cancanta ba, bisa ga tsarkin Allah. Mutum ya na iya cewa shi nagari ne amma Allah ya ce babu wani mai aiki nagari" (Romawa3:12b) wani kuma yana gani kamar shi yana ruyuwar adalci, amma Allah ya ce "Babu wani mai adalci, babu ko daya (Romawa 3:10). Wani kuma yana cewa zai tsira domin yana kiyaye dokokin Allah. Allah kuwa ya ce.

> Mutum ba zai samu kubuta ta wurin sharia'a (Galatiyawa 2:16a)

Ba Shakka, babu yadda mutum zai iya kubuta daga hukuncin Allah (Romawa 3:23). Babu tsira daga shari'ar sa. Kowa mai laifi ne, kuma an hukunta kowa, zuwa mutuwa ta har abada a cikin wutar jahannama ko yaya mutum ya yi kokari domin ya tsira da ikon kansa ba zai yiwu ba. Ana nufin ba za mu iya kubuta daga shari' arsa ba? Ba haka ba ne! Allah yana da shiri guda daya domin samun tsira shine ALHERIN SA. Ka bi shirin alheri nan, ka same tsira, ko kuma ka ki bin shirin nan na alheri, sai ka fuskanci fushin Allah na har abada (yahaya 3:36)

## Labari Mai Dadi

Yayin da mutum yake nasa kokari don ya tsira daga hukuncin Allah, sai wani ya zo don ya kubutar da shi. Wannan mutumin shi ne Yesus Kiristi, dan Allah na musamman, ya mika kansa da marar laifi wanda ya cancanci ya dauki hukuncin mutuwa da aka yanke wa mutum. Yahaya mai baftisma ya yi Magana game da wannan mutum na musamman, wato Yesu Kiristi, ya ce.

> Kun ga, ga dan Rago na Allah mai dauki da zunubin duniya (Yahaya 1:29b)

Manzo Birtus ya kara da cewa ya dauki horon zunubinmu.

> Shi da kansa ya dauki zunubanmu a Jikinsa a kan gungume (1 Bitrus 2:24).

Manzo Bulus ya ce:

> Amma kuwa Allah ya tabbatar mana da kaunar da yake mana, wato tun muna masu sunubi, Almasihu ya mutu dominmu (Romawa 5:8). Needs amplification ---- Christ dies [as substitute]

> Almasihu ya riga ya biya hakin zunubinmu sau daya tak, ba kari. (Ibriniyawa 9:12)

## Ya Dadin Labarin Nan Mai Dadi Yake?

An biya hakin zunubinmu, wato mutuwa, sau daya tak. An kawas da damuwar da ke tsakanin Allah mai tsarki da kuma mutun mara adalci. Zunubi ne ya raba tsakanin mutun da Allah (Ishaya 59:2). Yesu Kiristi ya kawas da wannan damuwar wurin yardarsa ya mutu a kan giciye. Wannan mutuwa da Yesu Kiristi ya yi a kan gicciye ta kawas da la' anar da aka dorawa mutum domin bai iya kiyaye dokar Allah ba. Kiristi ya fanshe mu daga shari' a ta wurin zama la'ananne domin mu, gama an rubuta cewa:

> Duk wanda aka kafa jikin itace la' ananne ne (Galatiyawa 3:13b)

Yesu Kiristi kadai, ba tare da wani kari ba, shi ne ya kawo salama tsakaninmu da Allah (I Timoti 2:5). Wannan baban bangon, wato yadda mutum ya kasa yin biyayya da umurin Allah, da kuma kokarin da mutum yake yi don ya ceci kansa duk Yesu kirsiti ya kawas da shi a kan gikiye.

> Ya kuma yanke igiyan nan ta shari' a da ta daura mu da dokokinta, ya dauke ta ya fake ta a kusa a jikin gikiyensa (Kokosiyawa 2:14)

Dominm Almasihu shi ne salamar mu, shi wanda ya mai da yahudawa da al' ummai daya. Wato ya rushe katangan nan da ta raba su kan gaba har ya soke shari'an nan mai umurni da dokoki, ta wurin ba da jininsa (Afisawa 2:14, 15a)

Tun mauna masu zunubi, Almasihu ya mutu domin mu (Romawa 5:8)

## Fitar Dab a Za 'a Manta Ba

Yi tunnani baya can game da Jirgin kasa da ya kama hanyar zuwa wurin da aka tara wadanda za'a kashe. Bayan saurayin nan mara laifi ya bad a ransa, akwai sharadi daya da alkalin ya ba wandanda suke so su fita daga cikin jirgin cewa, dole su fita ta wata kofa ta musamman. fita ta wannan kofa tana girmama mutuwar da mutumin nan mara laifi ya yi a madadinsu. Fitar da za a dinga tunawa! Yi tunani game da abin da mutanannan wadanda da za'a kashe suke tunani a zuciyarsu, su wadanda suka yi biyayya da umurnin alkalin suka fita ta kofar samun yanci.

An kamanta, Allah ya bada umurni daga kotunsa a can sama sharadi daya da ya bayar wanda za bi don ya samu karbuwa a wurinsa shi ne a shiga wurin sa ta hanya DAYA. Babu makawa game da wannan hanya. Abin da Allah ya fadi ba a sake shi. Dole mutane su fito ta kofa daya, Duk wanda yake so ya shiga, dole ne bi ta kofar da Allah ya shirya.

## Hanyar Shiga Sama

Game da sharadin da Allah ya bayar, Yesu Kiristi shi kansa ya yi Magana ya ce:

Ni ne hanya,ni ne gaskiya , ni nekuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurin na (Yahaya 14:6).

Luka Ya Kara Da Cewa:

Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk Duniyan nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto (Ayukan manzani 4:12).

Wannan yana nanata cewa, ban da Yesu Kiristi, ba wani dan adam da zai iya samun ceto, ko wani da zai iya shigan sama. Yesu Kiristi ya fada,shi da kansa. Babu wata gajerar hanya. Abin da Allah ya fada ba wasa yake ba. Ka bi kofar, ka shiga, ko kuma a rufe ka yi waje har abada ba za ka shiga sama ba.

## Yadda Za'a Iya Samun Ceto

Hanya daya ce tak zuwa sama, wato ta wurin Yesu Kiristi. Yesu Kiristi ya ce.

> Ni ne kofar, kowa ya shiga ta wurin na zai sami ceto (Yahaya 10: 9a)

Ta yaya mutum zai iya shiga kofar da ba iya gani ba? Tunda Yesu Kiristi shi ne kofar; hanyar kadai da mutum zai iya bi ya shiga ita ce ta wurin bangaskiya cikin Yesu Kiristi shi kadai. Kofar daya, bangaskiya daya cikin Kiristi kadai. Yaya yawan bangaskiyar da ake bukata kafin a sami ceto? Ko "yar karama ce kamar kwayar mastad" (Matiyu 17: 20)

**Misali na bangaskiya:** A cikin Tsohon Alkawari, mutanen Israila sun yi wa Allah rashin biyayya, Allah kuwa cikin aikata gaskiyarsa ya aika da macizai masu zafin dafi cikin jamma'a (Littafin Kidaya 21:6). Macizan kuwa suka sassari Israilawa da yawa kuwa cikin wahalar da suka sha suka furta zunubinsu ga Allah. Allah ya na iya barin mugayen macizan nan su kashe duk Israilawan nan marasa biyayya, amma ba yi haka ba. Maimakon haka, me Allah ya yi? Cikin alherinsa wanda ba kamarsa, ya cewa.

> Ka kera maciji da tagulla, ka sarkafa shi a bisa itace, Duk wanda maciji ya sare shi, idan ya dubi maciji na tagullar Zai ruyu (littafin Kadaya 21:8).

Sai Musa ya yi yadda Allah ya umurce shi. Ka gani, Musa ya bi umurnin da Allah ya ba shi daidai, sai ya ragewa Israilawa su bi umurnin Allah daidai ta wurin Musa. Suna da zabi, ko su yi abin da Allah ya ce su yi cikin sauki, ko kuma macizai su sare su har su kai ga mutuwa.

Ba shakka, duka wadanda ba su yi shakkar alherin Allah ba, ko hikimansa ba, ko ba su yi gunaguni game da umurnin nan mai sauki da Allah ya bayar ba, sai dai kawai suka dubi macijin da Musa ya kera, sun rayu (Littafin Kidaya 21 :9). Abin al'ajabi, abin

mamaki yadda alharin Allah yake da sauki ga Israilawa, da sauki sosai yadda tsofoffi da yara duka za su iya duban macijin su rayu.

Babu wani irin aiki da za a kara a kan wannan umurni na alheri. Allah ba ya bukatar wadansu alkawura, ba wani mika kai, ba wani mika kai na jamma'a, ba baftisma, ba'a bukatar zakka, wanna ba karamin alheri ba ne daga kotun Allah mai kauna. Wannan Allah wanda ya ba Musa umurni " yan dubban shekaru da suka wuce, shi ne ya sake ba da yadda mutum zai fita daga cikin halin kakani kayi da yake cikin.

## An Daga Dan Mutum Sama

> Kamar yadda Musa ya daga macijin nan a jeji, haka kuma dole ne a daga Dan Mutum, domin duk wanda ya gaskata da shi ya sami rai madawwami (Yahaya 3:14,15).

An daga Yesu Kiristi a kan gicciye lokacin da aka gicciye shi. Kamar yadda Israilawa suka dubi macijin da Musa ya daga sama zaka iya duban gicciyen, kuma ta wurin bangaskiya cikin Yesu Kiristi kadai za ka iya samun tabbaci daga wurin Allah shi da kansa, cewa kana da rain na har abada.

A cikin jeji, za su dubi macijin ne, Menene amfanin duban macijin? Ba komi ba ne.sai dai, gaskantawa ne kawai. Haka kuma ina amfanin gaskantawa?" gaskanta da Yesu Kiristi. Ceto nan da Allah ya bayar a cikin jeji a lokacin can yana da sauki samu a lokacin, haka kuma Allah ya bada ceto cikin sauki yanzu. Allah ya sa abubuwa su zama da sauki, sai kuma shaidan da masu yi masa hidima suka sa alherin ceto da Allah ya bayar ya zama da wuyar ganewa. Ceto abu ne mai sauki, mai sauki, mai sauki kamar a ce "ka bada gaskiya gare shi"; ba "ka bada gaskiya a yi maka baftisma"' ba ''ka baba gaskiya ka fara zuwa wata Ikilisiya''; ka, ba ''ka baba gaskiya ka kuma cigaba da ba da gaskiya;'' ba, ba ka baba gaskiya ka tuba, ka kuma sake ba da gaskiya;'' ba, ba ka baba gaskiya ka sa kiristi ya zama Ubangijka shi Ubangiji ne tuntuni. Babu wani abu da ake yi don kara bangaskiya. Allah ya riga ya ga ya mana dalla dalla yadda za mu iya samun ceto.

> Wanda ya gaskata da Dan. Yana da rai madawwami. Wanda ya ki bin Dan kuma. ba zai sami rai ba. Sai dai fushin Allah ya tabbata gare shi (Yahaya 3:36).

Saboda kaunar da Allah ya yi wa duniya har ya ba da makadaicin Dansa, domin duk wanda ya gaskata da shi kar ya halaka, sai dai ya sami rai Madawwami (Yahaya 3:16).

Amma an rubuta wadannan ne, domin ku ba da gaskiya, Yesu shi ne Almasihu, Dan Allah, ta gaskatawa kuma ku sami rai a cikin sunansa (Yahaya 20:31)

## Amincin Allah

Ko zai yiwu Allah ya yi karaya? Babu.

Allah ba kamar mutum ba ne, da zai yi karyaba (Litttafin Kidaya 23:19)

Idan Allah ya ce'' wanda ya gaskanta da Dan yana da rai madawwami (Ya kuma ce haka :Yahaya 3:36), abin da yake nufi ke nan. Idan ya ce'' duk wanda ya gaskata da shi (Yesu Kiristi) kada ya hallaka'' (kuma ya yi: Yahaya 3:16). Yana nufin cewa duk mutumin da ya gaskiya ga Yesu Kiristi ba zai shiga gidan wuta ba. Abin ba wuya. A daya gefen kuma, idan Allah ya ce, "Duk wanda ya dada gaskiya cikin Yesu Kiristi, ya sa a ka yi masa baftisma, ya kuma mika kansa gare shi ba zai hallaka ba, gara ka yi wadannan abubuwa idan ka taba begen samun rai madawani. Mum gode masa domin bai taba fadin wadanna abubuwa haka ba. Akwai wani abu da ya fadi a fili a cikin maganarsa.

A gaskata da Ubangiji Yesu, za ka sami ceto (Ayyukan Munzanni 16:31).

Wannan shi ne alherin Allah.

## Babbar Shawara Da Za Ka Yanke

Kana iya yanke shawara yanzun game da abin da zai sake rayuwarka har abada. Ta yaya? Ta wurin gaya wa Allah Uba cewa yanzun nan kana bada gaskiya ga Dansa wanda aka daga a kan gicciye don ya mutu a maimako ka. za ka iya gaya masa da bakinka, ko kuma cikin zuciyarka. Da zarar ka bada gaskiya ga Yesu Kiristi shi kadai, ka yi biyayya ga maganar Allah. Daga wanna lokacin mu'ujjizar ceto ta fara ke nan.

Wannan babban lokaci ne a cikin rayuwarka! Rai wanda aka cece shi ta wurin alherin Allah har abada.

Domin ta wurin alheri ne Aka cece ku (Afisawa 2:8).

Wadanne ne wadannan mu'ujjizan? Allah a madadin bangaskiyarka mara karfi, da rubabben adalcinka, ya baka adalcin cikakke (Romawa 3 :22) wanda da shi ne ake auna gaskiya. Haka kuma ya ba ka ransa madawami (Yahaya 3:36). A wannan lokacin kana da adalcin Allah. Kana kuma da ransa a cikinka. Wadanna kyautai na alheri daga wurin Allah da ka samu karo na farko a rayuwarka ya sa za ka iya zama tare da Allah a same har abada.

Menene ka yi don ka samu wadannan abubuwa? Ba kome. Saboda haka za ka iya zartas da cewa ba wani abu da ka yi, ko wani aiki da ya sa ka iya samun ceto sai dai wurin alherin Allah ne ka samu ceto. Ba wani abu da za ka iya yi don ka inganta abin da Allah ya yi. Abin da Allah ya yi ba'a sake shi (Roman 11:29).

Wannan shi ne labari mai dadi wannan kyakkyawan zarafi ne, zabi ya rage naka. Ta wurin bangaskiya cikin Yesu Kiristi kadai ake samun ceto. Wannan ita ce kadai hanyar da Allah ya tanada don tsira. Ko ka karbi alherinsa ya sake ka, ko kuma ka ki karbar alherinsa ka fuskanci sakamako na mutuwa to har abada.

Abin da Allah ya zartas, ya zauna ke nan:

> Wanda ya gaskata da Dan, yana da rai madawwami. Wanda ya ki bin Dan kuma, ba zai sami rai ba, sai dai fushin Allah ya tabbata a gare shi (Yahaya 3:36).

Zabi ya rage naka; saboda kai muke yin wannan addu'a dominka.

*Ya Ubanmu na cikin sama, muna gode maka domin kyautar alherinka, Danka wanda aka gicciye shi, mun gode domin ka sa samun ceto ya zama da sauki, kuma kowa yana iya samu Muna addu'a domin duk wadanda suka karanta sakon bisharar nan kuma ba su kai ga yanke shawara game da rayuwarsu ba. Ka sa su samu cikakkar ganewa game da sakamakon da zai biyo baya idan suka karbi kyautarka ta ceto na har abada,*

*ko kuma sa su karbi ceton nan. Uba, idan ka kalubalanci duk wanda bai bada gaskiya ga Yesu Kiristi ba ya yi tunani mai zurfi a kan sakon nan. A cikin suna Kiristi Amin.*

## Ga Wadanda Suka Gaskanta

Allah ya ce ku yi girma cikin alheri (2 Bitrus 3:18). Yana so ku yi marmarin koyaswa mai kyau (1 Bitrus 2: 2). Idan ka na so ka samu wannan "yar takarda da kuma wadansu littattafai da za su taimake ka cikin rayuwarka ta ruhaniya ba tare da ka biya kome ba, sai ka tuntubi adireshen bayan littafin.

**Bukatar addua'** (Domin masu bada gaskiya kadai)

> Ku lazamci yin addua, kuna zaune a fadake a kanta sosai, tare da gode wa Allah. (Kolosiyawa 4: 2)
>
> Addu'ar mai adalci tana da karfi aiki kwarai da gaskiye (Yakubu 5 : 16b).
>
> Mu ma ku yi mana addu'a Allah ya bude mana hanyar yin maganarsa, mu sanar da asirin Almasihu (Kolosiyawa 4:3)

---

## Sayi Gaskiya Amma Kada Ka Sayar la Ita

(Karin Magana 23: 23a).

Ko ka san koyaswa mai kyau ta Littafi Mai Tsarki Lu'u ne na ruhania? Ba shakka tarihin Ikilisiya ya numa yadda yake da wuya kwarai a samu koyaswa mai kyau, musamman a cikin Ikilisiyoyin zamani! Saboda Haka lokacin da Allah cikin yalwar alherinsa ya bi dam u cikin maganarsa mai daraja, mai gaskiya, mara kuskure, ya kamata mu dauke ta da muhimmnci ba tare da ciccijewa ba. Littafi mai Tsarki akwati ne dauke da duk abin da ka ke bukata don jin dadin rayuwa ta kowane fanni-abokantaka, aure, kasuwanci, da kuma more harkoki da suke zuwa yau da gobe; saboda haka ka "sayi gaskiya" (ka kafu cikin maganar Allah) "Gama hikima ta ti lu'ul'ai cikin dukan abin da kake so ba kamar to" (Karin Magana 8: 11).

Gaskiya: Tun da ya ke ba sharia ke iko da ku ba, ALHERIN Allah ne (Romawa 6:14b).

---

"Amma ku karu da alherin Ubangijinmu, Mai Cetonmu Yesu
Almasihu da kuma saninsa Daukaka ta tabbata a gare shi a yanzu,
Da kuma har abada. Amin"
(2 Bitrus 3: 18).

**Idan ka na so ka samu wanna dan littafi ko kuma wadansu kamarsa, sai ka rubuta zuwa ga wuraren nan guda biyu.**

A Afirika:
Grace Evangelistic Ministries
P.O.Box 583
Jos, Plateau State
Nigeria.

Darlington
dekwae@yahoo.com